**BINCIKE AKAN ZUBAR DA JINI**
**BAYAN HADARI A DUNIYA**

**Bayani ga mara lafia, ko danginsa, ko kuma wakilansa don neman amincewa da gudanar da binciken.**

**Wannan asibitin na cikin cibiyoyin nazari a duniya don neman hanyoyin rage zubar da jinni bayan hadari.**

**(1) Mun sanya ka a cikin wannan binciken**
**(2) Muna son mu sanya ka a cikin wannan binciken**

**(3) Muna son mu sa ------------------------------ (sunan mara lafiyan) a cikin wannan binciken.**
*(a yi alama a kan wanda ya dace)*

**ABIN DA YA KAMATA A SANI A KAN WANNAN BINCIKEN**

Wannan kasidar za ta yi bayani dalla-dalla a kan makasudin wannan binciken, da alherin da ke cikinsa, da kuma aibin da kan iya faruwa a lokacin binciken.

A wannan asibitin , akwai matakai na gaggawa da akan dauka don ganin an ceto wadanda suka yi hadari kuma suna zubar da jini mai yawa. An kaddamar da wannan bincike ne don gano hanyar da ta fi dacewa wajen maganin wannan matsalar.. Muna fatar yin anfani da wannan magani mai suna Tranexamic acid zai taimaka wajen toshe hanyoyin zubar da jini, wanda kuma zai rage zubar da jinin. Samun haka zai kawo ragowar zubar da jini, ya kuma rage bukatar karin jini bayan hadari. Amma kuma ya kyautu a san cewa tana yiwuwa wannan maganin ya kawo taruwan gudan jini a inda ba a bukatarshi a cikin jikin danAdam. Fatarmu a nan ita ce Allah ya sa fa'idar amfani da maganin ta fi ta duk wani aibin da ke ciki. Za a so mai karatu ya karanta sauran bayanai a tsanake, ya kuma tambayi likita don neman karin bayani a kan duk wani abun da ya shige masa duhu.

**(1) Me yasa aka kirkiro wannan binciken?**

Zubar da jini mai yawa , na iya kawo yankewar jini bayan an yi rauni wanda kuma shi ne babban musabbabin mutuwa. Yana da kyau a gano hanyoyin rage wannan zubar da jinin.

**(2) Mene ne makasudin yin wannan binciken?**

Wannan magani Tranexamic acid, an dade ana amfani da shi a wajen manyan ayyukan fida kamar aiki a zuciya wadda ita ce kusan maraya. Ana son a jaraba amfani da wannan maganin a ga ko zai kawo rage zubar da jini (da kuma bukatar karin jini) bayan an yi rauni. Shi wannan magani Tranexamic acid, ba sabon magani bane, domin an dade ana amfani da shi a fannoni dabam-dabam na rage zubar da jini.

**(3) Wane ne ke gudanar da wannan binciken?**

Dokta----------------------------- ne yake da alhakin gudanar da wannan binciken a wannan asibitin.Ana yin wannan binciken ne tare da taimakon wadansu likitoci a jami'ar London.

**(4) Mara lafiya ba zai iya shiga cikin wannan binciken ba idan ya kasance a cikin wadannan:**

- Wadanda basu shekara goma-sha-shida da haihuwa ba
- Wadanda ba a samu kawo su asibiti ba sai bayan sa’a takwas da yin hadarin
- Idan a ra’ayin likita akwai wani dalilin da zai hana amfani da Tranexamic acid a kan majinyaci
- Idan a ra’ayin likitan, majinyacin dama yana bukatar shi wannan maganin(Traxenamic acid) ba tare da an yi wannan binciken ba

**(5) Mene ne ya wakana ko zai wakana a lokacin gudanar da wannan binciken?**

Za a yi wa mara lafiya dukkan abin da aka saba yi don maganin zubar da jinni, har da karin ruwan da akan yi a makwafin karin jini. Shi wannan magani ya kasu kashi biyu; daya yana dauke da ainihin maganin, watau Tranexamic acid, dayan kuma lami yake (watau baya dauke da maganin). Za a bayar da maganin na tsawon sa'a takwas a asibiti. Komfiyuta ce ta tantance irin maganin da a ka ba mutum a can Oxford ta kasar Ingila. Amma ko likitoci masu kulawa da mara ` lafiyan ba za su iya sani ba. Dukkan bayanan da aka tattara za a aika da su cibiyan bincike da ke London ba tare da an fallasa abin da ke ciki ba.

**(6) Shin akwai wani hadari wajen shiga wannan binciken?**

Shi wannan magani ana amfani da shi a wurare da dama, kuma har yanzun ba a samu wani tartibin bayani ba dangane da aibin da zai iya jawowa idan an yi amfani da shi na dan gajeren zango ba.

**(7) Mene ne alfanun da ke cikin kasancewa a wannan binciken?**

Muna fatar wannan maganin zai rage yawan zubar da jini (ya kuma rage bukatar karin jini). Ilimin da za mu samu a wannan binciken zai taimaka gaya ga duk mutanen da su ka ji rauni mai kawo zubar da jini a nan gaba.

**(8) Idan mutum na da tambaya ko neman karin bayani, wa zai tuntuba?**

Idan ana neman Karin bayani sai a samu Dokta----------------------------------

Ko kuma a tuntubeshi ta layin tarho kamar haka---------------------------------

**(9) Akwai bukatar mu boye wani bayani ?**

Duk wani bayani da aka bayar gameda mara lafiyar a sanadiyar rauni ko kuma yanayin raunin, za a adana shi cikin aminci. Ba wanda za a bari ya yi amfani da bayanin sai su likitocin da ke yin binciken da kuma mataimakansu

a can cibiyar binciken a London. Akwai hukuma ta musamman da take lura da wannan binciken tare da tabbatar da an yi binciken a kan ka'ida. Bayan kammala binciken da kuma nazarin bayanan, za a buga rahoto a mujalla ta musamman domin karuwan likitoci da sauran ma'aikatan lafiya a duniya. Dukkan abinda za a buga, ba zai kunshi bayanin da zai sa a gano wanda ya shiga binciken ba.

**(10) Ana iya gama binciken a kan majinyaci da wuri kuwa?**

Maganin da ake bayarwa yayin wannan binciken ana bayar da shi ne a cikin gaggawa. Muna fatar za a amince mu tara bayani a kan majinyacin. Amma idan akwai wani tsaiko a kan yin haka, to sai a sanar da likita..

**(11) Akwai wani Karin bayani da ya kamata a sani?**

- Wannan binciken, Jamia'r London da Hukumar Lafiya ta Duniya (WHO) ne suka dauki nauyin gudanar da shi, ba kamfanin Tranexamic acid ba.
- Cibiyar binciken (watau London School of Hygiene and Tropical Medicine) za ta dauki alhakin biyan duk wani abin da ka iya tasowa na ka'ida, ga wani ko wasu a yayin wannan binciken.

---

Idan akwai wata tambaya a kan shiga cikin wannan muhimmin bincike a kan zubar da jini bayan hadari, to sai a tuntubi:

(A SANYA BAYANI A KAN ASIBITI A NAN)

STUDY CO-ORDINATING CENTRE
International Study of Bleeding After Injury, Room 180
London School of Hygiene & Tropical Medicine
Keppel Street
London WC1E 7HT
United Kingdom
Tel +44 20 72 99 468
WWW.CRASH2.LSHTM.AC.UK

**BINCIKE A KAN ZUBAR DA JINI**
**BAYAN HADARI A DUNIYA**

**TAKARDAR AMINCEWA**
(idan akwai bukata)

---

**Na fahimci manufar wannan bincike, kuma na amince**:

(1) in shiga ciki
(2) a yi amfani da bayani a kaina a yayinda nake jinya, wajen wannan bincike.

**Ko kuma idan ba majinyacin ba ne,**

(3) mai jinyar da aka ambaci sunansa a nan kasa, ya shiga cikin binciken
(4) a yi amfani da bayani a kan farfadowar majinyacin a wajen wannan binciken

Sa hannu ----------------------------------------------

Kwanan wata-----------------------------------------

Sunan majinyacin-------------------------------------

Sunan Likitan da ya nemi amincewa ------------------------------------------

Sunan wanda ya amince---------------------------------------------------------

Dangantakar wanda ya amince da majinyacin----------------------------------